# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Ni ma ɗan Adam ne: 'Yan Afirkan da ke fama da taɓin hankali
## Kashi na biyar: Hanyar samun waraka


Wanda ya rubuta: Chrispin Mwakideu

Wanda ya fassara: Yusuf Idris

Wadda ta tace: Halima C. Schmaling


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Duduwa: | 'yar shekara 35 |
| Maude: | ɗan shekara 65 |
| John: | ɗan shekara 25 |
| Jane: | 'yar shekara 25 |
| Fasto: | ɗan shekara 40 |
| Dije: | 'yar shekara 19 |
| Dorathy: | 'yar shekara 18 |

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin shirinmu na “Ji Ka Karu” kashi na biyar, wanda muke kawo muku a kan mutane masu taɓin hankali a nahiyar Afirka. A cikin shirin da ya gabata, kun ji yadda jama’a suka ƙona wa Duduwa gidanta, wai don suna zargin ta zama mayya saboda ɗanta Musa yake fama da taɓin hankali.

Ku kasance da mu a cikin wannan shirin mai taken “Hanyar samun waraka”. Za mu faro ne daga ƙauyen su Duduwa inda a halin yanzu dai ba ta da gida, wanda ya sa ta tafi wurin mutum ɗaya da ta yarda da shi a ƙauyen, wato mai maganin gargajiyan nan Maude.

**Fitowa ta 1: A ƙauye**

**Maude:** Duduwa, ashe abin da ya faru ke nan?

**Duduwa:** Wallahi Maude, na rasa komai, amma na gode wa Allah cewa Musa baya cikin ɗakin. Shi ma da na rasa shi ke nan.

**Maude:** Iyayenmu ne suka kare shi.

**Duduwa:** Maude, yau buƙatata ɗaya ce kawai. Tun da na rasa duk abin da na mallaka a wannan wutar, ba abin da zan zauna in yi a nan. Ina da niyyar in tafi birni. Ina da wani ɗan’uwa a can da yake aiki kuma zai iya taimako min a kan Musa kafin in gina nawa gidan.

**Maude:** To, yanzu kina so in ranta miki aron kuɗin mota ke nan.

**Duduwa:** Lallai ka cika cikakken mai baiwa. Yaya aka yi ka san abin da nake so? Har ka san matsalar da ke tafe da ni tun kafin in faɗa maka.

**Maude:** To ai wannan ba wani abu ba ne na yin duba kafin mutum ya gane haka. An ƙona miki gida, ba ki da wasu kuɗaɗe a hannunki, sannan ga shi sai kin yi tafiya mai tsawon gaske kafin ki je birni. Ai ba da ƙafa za ki je ba ko?

**Duduwa:** A'a, ai haka zai yi wahala. Ka ga ma idan muka je can, sai in kai Musa wurin likita ya duba shi. Ko ya ka gani?

**Maude:** Ina ganin ya kamata ki yi duk abin da ya dace don ki taimaki ɗanki. Yaro ne da ya kamata a taimake shi, kuma ina jin takaicin cewa na kasa taimakonshi. Wataƙila za su iya ganin abin da ke damunshi. Maganar gidanki kuma, ai na san waɗanda suka ƙona miki shi.

**Duduwa:** Mene? Kana nufin da gangan aka ƙona min gidana? To me ya sa? Ni ai ba ni da matsala da kowa!

**Maude:** Haka ne, amma su suna jin haushinki ne, Duduwa. Wasu daga cikinsu sai da suka zo wuri na tukuna kuma sai da na gargaɗe su a kan cewa kada su aikata haka. Wai suna zarginki da yin maita.

**Duduwa:** Ni, mayya? Wannan wace irin magana ce! Wayyo Allahna! Wato sun so su kashe ni ne lokacin da suka zo suka ƙona min gida. Suna tunanin cewa ina ciki ne?

**Maude:** Haka ne. Amma kuma idon iyayenmu na kallonki. Shi ya sa na yarda da shawararki na barin ƙauyen na ɗan wani lokaci. Ni zan san abin da zan yi a kan wannan maganar.

**Duduwa:** Maude, ban taɓa cutar da kowa ba. Me ya sa mutane suke so su ga na mutu? Me ya sa? Ni ba abin da ke gaba a da ta fi maganar ɗana Musa.

**Maude:** Wasu daga cikinsu ma tunaninsu shi ne cewa ke kika kama ɗanki. Sun zarge ki da abubuwa da yawa. Amma dai wannan ba shi ne abin da za mu tsaya muna magana a ka ba. Ni na san ko ke wace ce, kuma ba ni da wani shakkun cewa ke ba mayya ba ce. Ya tabbata cewa iyayenmu ne suka sa kika fita daga gidanki, kika je ɗiban itace.

**Duduwa:** A'a! Amma abin ya ba ni mamaki. Yaya za a yi mutane su zama masu mugunta?

**Maude:** 'Yata, zamanin nan namu ya canza. Wannan duniya sai a hankali. To yanzu dai ga kuɗin nan, ki kama hanyarki ta zuwa birni.

**Duduwa:** Maude, waɗannan tsabar sun yi yawa. Ba ka da takardun kuɗi ne?

**Maude:** Ba na karɓar takardun kuɗi, 'yata.

**Duduwa:** To, ban sani ba. Kakannin-kakanninka ba sa son takardun kuɗi ne?

**Maude:** A'a! Amma dai akwai jabun takardun kuɗi da ke yawo cikin 'yan kwanakin nan. Amma yana da wuya a yi jabun tsabar kuɗi. Yanzu sai ki kama hanya, kuma ina yi miki fatan lafiya, Allah ya kare ki.

**Duduwa:** Maude, ba ni da abin da zan ce maka, sai dai Allah ya biya ka. Na gode, Allah ya saka da alheri!

**Mai ba da labari:**

Al'adu a nahiyar Afirka kan shafi hanyoyin gudanar da rayuwa a yankin. Kuma gaskiya ne cewa har yanzu masu maganin gargajiya suna taka muhimmiyar rawa, musamman ma a ƙauyuka inda ba su da asibitocin kula da marasa lafiya.

Yanzu bari mu ƙara komawa wajen John wanda matarshi Jane ta haifi 'ya mace ba tare da wata matsala ba. Yanzu dai iyayen 'yar, tare da paston nan sun koma gida, amma dai har yanzu shi paston na cikin damuwa a kan niyyar da John ya yi na kashe kanshi. Bari mu kasance tare da su a cikin murnar da suke yi da kuma ruɗun da suka samu kansu.

**Fitowa ta 2: A gidan John**

**Jane:** John, don Allah ko za ka miƙo jinjirar nan, ina ganin tana so ta sha nono ne.

**Fasto:** John, ka ji abin da matarka ta ce?

**John:** Don Allah ku rufe min baki! A'a, ni ba zan iya jure wa wannan hayaniyar ba, tana nema ta sa ni hauka. Don Allah kowa ya yi shiru.

**Fasto:** Sssshhhh... Yi shiru 'yammata. Babanki ya ɗan gaji ne. Amma ba ya yi niyyar ya ba ki tsoro ba ne. Zo nan mu gani. Yauwa, ya yi daidai.

**Jane:** Na gode, Fasto. Don Allah ka yi wa John magana. Ba zan iya jure wa abin da yake yi ba. Ban san abin da zan yi ba. Ko sunan da za a sa wa yarinyar ma bai faɗa ba!

**Fasto:** John, mu ɗan je waje mu yi magana mana. Ba za mu daɗe ba.

**John:** Me kake nema a wurina ne, Fasto? Ba zan iya ba ka komai na baiwa ba, na rasa aikina. Ba zan iya yin waƙa ba a kwaya ba, na rasa muryata. Ba zan iya yin addu'a ba, na rasa imanina. To mene ne kuma?

**Fasto:** Don Allah John, mu ɗan ba Jane da 'yarka wuri su ɗan huta. Ba na son komai daga wurinka. Ni dai buƙatata kawai shi mu ɗan je waje mu zagaya?

**John:** Mu ɗan zagaya? Kana nufin ni da kai mu ɗan zagaya?

**Fasto:** Abin da nake nufi ke nan. Mu ɗan zagaya da kai. Kar ka damu da canza matsayin ka samu a yanzu. Mu dai fita waje mu ɗan sha iska mai daɗi, ya ta taimaka maka bayan wahalar da muka sha a asibiti da Jane.

**John:** Shi ke nan, mu je! Amma ba zan iya zuwa da nisa ba.

**Fasto:** Ba wani abu ba ne ai, mu je iya inda za ka iya zuwa.

**Mai ba da labari:**

Ba tare da ma ya sani ba, John ya ɗauki mataki na farko na samun waraka. Wannan paston ya fara ɗaukar matakin warkar da John. Kar ku manta, kwana da kwanaki dai John ba ya nuna sha'awa a kan komai. Ya kai wani matsayi da ya kusa kashe kanshi.

A yayin da mutanen biyu suka fita waje don su sha iska mai daɗi, a wani ɓangaren garin kuma Dije ta ci gaba da neman ƙawarta Amina. Kwana da kwanaki ba ta gan ta ba saboda haka sai ta shiga nemanta a ko'ina. Har ma ta kai wa jami'an 'yan sanda rahoton cewa ta ɓace. Amma har yanzu, ba

wanda aka samu da ya gane hoton Amina da Dije take nunawa. A yanzu haka Dije tana barin wani gidan rawa ne inda ta je don samu ta ɗan sarara. Tana dai tare ne da wa ta ƙawarsu mai suna Dorathy.

**Fitowa ta 3: A hanya**

**Dorathy:** Dije, ashe dai kin iya rawa sosai, ban sani ba.

**Dije:** Haba, Dorathy, ki daina faɗin haka. Ai kowa ya iya, sannan kuma na ji daɗina. Ina ma a ce Amina tana nan. Abin yana damuna sosai ganin cewa ban taimake ta yanda ya dace ba.

**Dorathy:** Ki daina zargin kanki. Ba yadda za ayi ki tsai da wani daga zama mahaukaci! Ko yaya aka yi, haka sai ya faru. Saboda haka ki manta da shi kawai ki ci gaba da rayuwarki.

**Dije:** Ai a nan matsalar take, ba zan iya mantawa ba. Amina yarinyar arziki ce. Na san ta, kuma duk ta fi kowa ƙoƙari a cikinmu. Ba ki ganin babban rashin da aka yi?

**Dorathy:** A'a! Maganar gaskiya ma ita ce, da ma ni ba na sonta. Gaskiya abin takaici ne cewa yanzu ta haukace kwata-kwata, amma kuma sai me? Akwai ɗaruruwan mahaukata kamar ta, sannan kuma ba wanda ya damu.

**Dije:** Amma me ya sa, Dorathy? Me ya sa ba ma yin wani abu don mu taimaka wa waɗannan masu taɓin hankalin? Da ke da ni mun san cewa wasu daga cikinsu suna buƙatar kulawar da ta dace kawai, sai ki ga sun warke gaba ɗaya.

**Dorathy:** Me ya sa, Dije? Kar ki zama ’yar ƙauye mana. Ke kin san cewa muna da matsaloli na cututtuka da suka fi na masu taɓin hankali.

**Dije:** Na yarda da ke, Dorathy, da kika ce muna fuskantar babban ƙalubale a kan kiwon lafiya. Amma kin san wani abu? Ya kamata a ce taɓin hankali yana daga cikinsu. Ina gudanar da wani bincike, kuma na gane cewa ɗaya daga cikin kowane mutum huɗu zai iya samun taɓuwar hankali a rayuwarshi. Wannan kamar yadda Kungiyar Lafiya ta Duniya ta fitar ke nan. Amma kin san wani abu? A duk duniya, kashi uku kawai ake keɓewa daga kuɗin da ake kashewa a kan lafiya don kula da masu taɓin hankali.

**Dorathy:** Ashe, haka ne?! To gaskiya, ni ban san da haka ba. Ɗaya daga cikin kowane mutum huɗu, ai kuwa haka na da yawa! ... Kalli, muna maganar masu taɓin hankali: Kalli waccan mahaukaciyar da ke zama a gaban shagon can. Tana ɗaya daga cikin huɗun.

**Dije:** Wace mahaukaciya? A ina?

**Dorathy:** Ga ta can! Ko riga ma ba ta da shi a jikinta. Na san kuma sanyi kuwa na damunta!

**Dije:** Wayyo Allahna! Me zan gani haka. *Oh no.* Waccan ai Amina ce!

**Mai gabatarwa:**

Da haka kuma muka kawo ƙarshen wannan shiri na yau. Me zai faru nan gaba bayan Dije ta ga Amina a cikin wannan hali na ƙasƙanci da takaici da ma tausayi? Me zai biyo bayan fitar da fasto da John suka yi domin zagayawa?

Sannan kuma, me Duduwa da ɗanta za su tarar a lokacin da suka isa birni? Duk za ku ji waɗannan a cikin shirinmu na gaba idan Allah ya kai mu. Kafin nan kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo a dw.de/lbe domin sake sauraron wannan shiri da ma wasu. Kazalika kuna iya ziyartar shafinmu na Facebook. Sai mun sadu a shiri na gaba